## TSATTSARKAN MUTANE - Babi 1 - 6

Isra'ilawa sun bar bauta a ƙarƙashin Fir'auna zuwa samun 'yanci. A surori na biye za mu koyi abin da ake nufi da danganta da Allah. Abubuwan da aka yi a Sinai sun haɗa da saduwa da Allah, sabunta alkawari da ba da doka. Waɗannan abubuwa sun ba da misali iri biyu na dangantaka da ke tsakanin Allah da mutanensa waɗanda suke bukata su kasance zuciya mai biyayya kuma keɓeɓiya rayuka.

Fitowa 21-23 tarin dokoki ne da ake kira 'Littafin Alkawari' wanda ya ba da jagora da bishewa ga rayukan mutanen Allah a wancan lokaci.

# Babi na 1 Saduwa da Allah

**Fitowa 19:1-25**

TAMBAYOYIN TATTAUNAWA MINTI 30

**MANUFA:** Yayin da muna saduwa da Allah za mu koyi yadda za mu nuna halinsa a rayuwarmu.

A lokacin da Allah ya fara kiran Musa don ya je wurin Fir'auna ya fitar da Isra'ila da suke bauta a Masar, ɗaya daga cikin alkawuran shi ne mutane za su yi "sujada a kan wannan dutse"(Fitowa 3:12). Don haka a duk lokacin da Musa ya zo wurin Fir'auna, saƙon shi ne, "Ubangiji Allah na Ibraniyawa ya aike ni gare ka da cewa, ka saki jama'ar Ubangiji domin su yi masa hidima a jeji" (Fitowa 7:16; 8:1,20; 9:1, 13; 10:3).

Kalmar nan 'jeji' ba tana nufi hamada inda babu ruwa ba, amma wani lokaci yana nufin wajen kiwo inda babu mutane. Fitowarsu daga Masar wata uku ke nan suka iso Dutsen Sinai don su sadu da Allah su yi masa sujada. Muhimmin zarafi ne ga Isra'ilawa domin shiri na dukan abubuwan da za su faru nan gaba.

**Karanta Fitowa 19:1-9**

**Gayyatar Allah:**

1. Wane alkawari ne yanzu ya cika bayan Isra'ilawa sun yi wata uku da barin Masar (aya 1-2)? Dubi Fitowa 3:12.
2. Ta yaya Allah ya bayyana wa Musa abubuwa uku muhimmai da ya yi wa mutanensa (aya 4)? Waɗanne alkawura ne Allah ya yi kuma a kan waɗanne sharuda ne za su cika (aya 5-6)?
3. Da Allah ya gayyaci mutanen, me suka yi (aya 8)?
4. Ina manufan Allah a shirinsa da ya ya yi magana da Musa ta cikin girgije (aya 9)?

**Karanta Fitowa 19:10-15**

**Muhimmin shiri:**

5. Waɗanne abubuwa uku mutanen nan za su yi saboda shirin saduwa da Allah (aya 9-15)?
   Zai ɗauke su kwana biyu suna shiri. Me wannan ya nuna game da kular da za su yi a shirinsu?

CI GABA DA TAMBAYOYI

**Karanta Fitowa 19:16– 25**

**Allah ya yi Magana da mutanensa:**

6. Mecece alamar kasancewar Allah a kan dutse (aya 16, 18-19)?
   Me ya faru da mutanen saboda kasancewar Allah?

7. Wanene ya iya jagorantar mutane daga sansani zuwa inda za su sadu da Allah? Mecece muhimmiyar dangantakar da ya yi da Allah (aya 9, 20)?

8. Don me mutanen suka kasa zuwa kusa da dutsen don su sadu da Allah (aya 21-23)?

TAKAICIN KOYARWA MINTI 5

Wannan wani abu ne wanda mutanen Allah ba za su manta ba. A nan Allah ya sake tabbatar da sabuntar dangantaka da Isra'ila wanda za su waiwaya su duba saboda sanin asalinsu da kariya. Allah ne ya yi gayyata ta wurin Musa sai shi ya gayyaci dattawa da mutane.

Da yadda suka san amincin Allah -ya cece su, ya ɗauko su, ya kawo su kusa da shi - An gayyace su saboda su miƙa kansu don yin dangantaka ta musamman da shi (aya 5). A sakamakon wannan dangantaka, za su zama dukiyar Allah na musamman, mutanen -sa da suka zama dabam da sauran mutane. Za su yi masa hidima kamar firistoci da aka keɓe saboda yi masa hidima don cika shirinsa.

Wannan muhimmiyar saduwa tana bukatar mutane su yi shiri a hankali, su shirya kansu da 'tsabta' ciki da waje. Kwana biyu suna shiri, a kan rana ta uku Allah ya bayyana garesu. Akwai walƙiya da aradu da karan busar ƙaho. Dutsen ya girgiza sai mutane suka ji tsoron kasancewar wannan Allah Mai Iko Dukka, Mai Tsarki kuma. Musa kaɗai ne ya sami zarafin yin magana da Allah, ya iya yi wa mutane jagora daga sansani don su sadu da shi.

A cikin Almasihu, mu ma muna cikin masu gādon muhimmiyar dangantakan nan. Ta yaya za mu nuna kasancewar Allah da halinsa ga waɗanda suna kewaye da mu?

AYYUKAN YI MINTI 20

A rabu cikin ƙungiyoyi 2-3 don a tattauna a yi addu'a kuma.

1. Menene aikin masu bi a yau cikin shirin Allah?
   Yaya kake shirin zama ɓangaren waɗannan shirye-shirye?

2. An faɗa wa Isra'ilawa da su yi shiri sosai kafin nan su zo gaban Allah.
   Ta yaya kake ji wannan zai shafe mu a yau?

Karanta **Fitowa 20:1- 26** a makon gobe.
Ina amfanin waɗannan dokoki gare mu a yau?

**ADDU'A:**

* Gode wa Allah saboda muhimmiyar dangantaka da za ka yi da shi ta wurin Almasihu.
* Roƙi taimakon Ruhu Mai Tsarki ya taimake ka ka bayana halin Allah a rayuwarka na yau da kullum.

**HADDACEWA: Fitowa 19:5-6**